# Lokacin Aiwatarwa!

Mahalarta taron za su koyi yanda za su samar da shirin farko a kan tasu fafutukar wayar da kan jama'ar.

## Kayayyaki darasi

Takardar Darasin Wayar da kai a kan Rajin Kawo Sauyi

# Wani Shirin Kawo Canji!

## Kashi na Ɗaya

**Sanar da Ɗalibanka**

A cikin wasu daga cikin sauran harkokin da suka shafi ilimantarwar waɗanda a aka haɗa su da harkokin jama'a da siyasar da muka kammala tare, mun bincika fasaha daban-daban da ra'ayoyin da za su iya yin amfani wajen zama mai fafutukar kawo sauyi.

Mun gano matsalolin da suka shafi al'ummarka sannan kuma mun ƙara fahimtar wasu abubuwa game da ƙayyadaddiyar hanyar sadarwa da kuma kayan aikin watsa labari da za a aiwatar da sauyin.

Yanzu, lokaci ya yi da za a tattara waɗannan ra'ayoyin wuri guda sannan ka shirya taka fafutukar wayar da kan jama'ar tun daga farko har zuwa ƙarshe!

**Tattaunawa a Aji**

Ba tilas ba: Gabatar da wata sabuwar fafutukar wayar da kan matasan da ta dace wadda aka daidaita ta da / mahalarta taronka na cikin gida / abubuwan yankin. Shafukan yanar gizon Muryoyin Matasan (a cikin Ingilishi, Spanish, Faransanci, da Larabci) da Muryoyin Mutanen Duniya (idan za su taimaka, a cikin shafin yanar gizon, binciko kalmar "matasa") za su iya zama wani tubalin da zai tsima mutane idan ba ka tabbatar da wayar da kan da za ka zaɓa ba. Saki jiki ka gabatar da shafin yanar gizon wayar da kan mutane a kan allon majigin kamar yanda ka bayyana shi.

# Aiki

## Aiki

**Sanar da Ɗalibanka**

Ƙirƙiri wani rubutu da zai jero fafutukar wayar da kan jama'ar da kake so ka gudanar a cikin al'ummarka. Za ka iya haɗawa da rubutun da ka rubuta a wasu daga cikin harkokin ilimantarwar da suka gabata. Misali, za ka iya sanya bayanai game da matsalar da kake so ka yi magana a kai, ko kuma bayani game da al'adun mutanen da ka zaɓa don samun goyon baya wajen wayar da kan jama'arka tare da manufofin fafutukarka. Kana da mintuna 30 da za ka tsara wayar da kan jama'arka.

Ka ɗan amsa waɗannan tambayoyin:

1. Wace matsala ce kake so ka yi magana a kai?
2. Wace al'umma ce wannan matsalar ta shafa
3. Ta yaya kake so ka magance matsalar
4. Wane irin dandalin watsa labarai ne kake so ka yi amfani da shi wajen wayar da kan jama'ar da ke kewaye da sanadinka? Ta wace hanyoyi?
5. Shin akwai wata al'adar mutanen da kake so ka yi amfani da ita wajen wayar da kan jama'arka? Ta yaya?
6. Wa zai kasance a wajen goyon bayan hanyar sadarwarka?
7. Wane yankin jimla ne za ka ƙirƙirar a kan wayar da kan jama'arka?
8. Mece ce farfajiyar wayar da kan jama'arka?

Ka saki jiki don ka samar da ra'ayoyinka a Takardar Fafutukar Wayar da Kan Jama'a, ko kuma a wata takardar daban.

**Aiki**

Ba Mahalarta Taron Takardar Wayar da Kai a kan Rajin Kawo Sauyi

**Tattaunawa a Aji**

Yanzu, da bibbiyu da bibbiyu, za ka raba rubutun fafutukar wayar da kan jama'arka. Yi magana da abokin hulɗarka game da ɓangaren wayar da kan da ya fi burge ka!

**Tattaunawa a Aji**

Ba mahalarta taron damar mintuna 20 domin su raba wayar da kansu a tsakaninsu.

Wannan kayan karantarwar da Matasa da Kafar Watsa Labarai suka samar a Cibiyar Samar da Intanet &amp ta Berkman Klein; Jama'a a Jami'ar Harvard a ƙarƙashin lasisin Creative Commons Attribution-ShareAlike 4.0 International. Za ka iya yin amfani da wannan, har da yin kwafi da kuma shirya samar da ayyuka, ko kuɗi ko kuma wanda ba na kuɗi ba, kamar yanda ka siffanta. Matasa da Kafar Watsa Labarai a matsayin tushen da suka samar da ayyukan na ainihi da kuma raba wasu ayyukan da za su zo a gaba a ƙarƙashin sharuɗɗa ɗaya. Waɗannan da wasu ƙarin kayayyakin karantarwar su ma akwai su a intanet a Dandalin Kayayyakin Karatu da Rubutun Zamani na Berkman Klein.